Mala'iku ba sa shiga gidan da yake akwai kare ko hoto a cikinsa

Daga Abu Ɗalha - Allah Ya yarda da shi - daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Mala'iku ba sa shiga gidan da yake akwai kare ko hoto a cikinsa".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa mala'ikun rahama ba sa shiga gidan da a cikinsa akwai kare ko hoton masu rayuka; Hakan cewa hoton abinda yake da rai: Saɓo ne mai muni, kuma a cikinsa akwai kamanceceniya da halittar Allah, kuma hanya ce daga hanyoyin shirka, wasu daga cikinsu hoton abinda ake bautawa ne koma bayan Allah. Amma sababin hanuwarsu daga (shiga) gidan da a cikinsa akwai kare: Saboda yadda yake yawan cin najasa, kuma sashinsu an ambace shi Shaiɗan; mala'iku kishiyotin shaiɗanu ne, saboda munin warin kare; mala'iku suna ƙin mummunan wari, kuma su (karnuka) an yi hani daga kiwonsu; sai aka yi wa mai riƙonsu ukuba da haramcin shigar mala'ikun rahama gidansa, da sallarsu a cikinsa, da nema masa gafara, da sa albarkarsu gare shi da kuma cikin gidansa, da tunkuɗewarsu cutar Shaiɗan daga gare shi .

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/8950